# ALƘA'IDATUL MADANIYYAH

**Don koyarda karatun Larabci ga ƴan koyo**

Wannan tsari ne da ake bi a tsangayoyin Alƙur'ani da koyarda littattafan ilimi a Masallacin Annabi




**Dr. Abdulmuhsin bin Muhammad Alƙasim**
**Limami kuma mai huɗuba a masallacin Annabi**

بلغة الهوسا

# ALKA'IDATUL MADANIYYAH

Don koyarda karatun Larabci ga ƴan koyo

# ALKA'IDATUL MADANIYYAH

Don koyarda karatun Larabci ga ƴan koyo

Wannan shine tsarin da ake bi a tsangayoyin Alƙur'ani da koyarda littattafan ilimi a Masallacin Annabi

WALLAFAR

Dr. Abdulmuhsin ɗan Muhammad Alƙasim
Liman kuma mai huɗuba a masallacin Annabi

# BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHIM

## GABATARWA

Godiya ta tabbata ga Allah, kuma tsira da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad, da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka:

Haƙiƙa wannan al'ummar ta ɗaukaka ne da ilimi; kuma aya ta farko data sauko tana kwaɗaitarwa akansa; Allah Maɗaukaki ya ce:

﴿اقْرَأْ بِاسْمِ رَبِّكَ الَّذِي خَلَقَ﴾

{Kayi karatu da sunan Ubangijinka wanda yayi halitta} [Al-alaƙ: 1].

kuma saboda kasancewar haɗa baƙi yana daga cikin mafarin koyon ilimi; wannan yasa na tattara tushensa kuma nayi ƙoƙarin kewayewa da sauƙaƙawa da kuma samarda ƙwarewar karatu ga masu koyo, tareda taƙaita tsawon lokacin koyon karatun kuma nasa masa suna:

**((AL-ƘA'IDATUL-MADANIYYAH - DON KOYARDA KARATUN LARABCI GA 'YAN KOYO))**

Allah nike roƙo Ya amfanar da wannan littafin kuma Ya sanya shi don fuskarSa mai daraja.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhmmad da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya. .

Dr. Abdulmuhsin **ɗan** Muhammad Alqasim
Liman kuma mai Huɗuba a Massalacin Annabi mai alfarma.

Na kammala rubuta shi a ranar Sallar idin layya
Shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba'in da ɗaya bayan Hijra

## AIKIN DANAYI A CIKIN WANNAN LITTAFIN SHINE:

1. Na gina wannan littafin akan gini na ilimi, ina mai dogaro cikin yin hakan akan littattafan yaren harshen Larabcin.
2. Na sanya littafin ya ƙunshi dukkanin ƙa'idodin da ɗalibi yake buƙatar su.
3. Nayi shimfiɗa kafin kowane darasi, wacce ta ƙunshi yanda ake rubuta kowane harafi da sunansa da sautinsa.
4. Na kasa wannan littafin zuwa babi goma sha uku (13), a ƙarƙashin kowane babi sau da yawa akwai darussa.
5. A tsarin wannan littaffin, nabi hanyar data dace da hankali da bin matakai wurin koyarwa.
6. Na ƙulla alaƙa tsakanin kowane darasi da ɗan uwansa; don ɗalibi ya riƙa halarto da abinda ya gabata.
7. Na sanyama kowane babi manufofin ilimi da ake fatan samu a cikinsa; don ɗalibi ya cin masu su.
8. A farkon kowane babi, na bayyanama malami ababen dayake buƙata a cikinsa na hanyoyin karatu da sauran ababe.
9. Na tsara wata hanya gajeruwa wurin koyon karatu.
10. Na ware wasu babuka da darussa na musamman ga wasu ƙa'idodin karatu; don muhimmancin ƙwarewa akansu kuma domin ɗalibi ya kaucewa samun ruɗani a cikinsu.
    - A. Harafin Alhamzah; saboda Muhimmancinta da zuwanta tareda wasu haruffa da ake kira da suna haruffan illa a mafi yawan lokaci.
    - B. ((Alhamzatul-mamduda)); saboda haɗuwar harafin Hamzah guda biyu a cikinta, ko haɗuwar hamzah da alif.
    - C. ((Al-aliful-maƙsura)); saboda kama dayake da harafin ya'un a cikin rubutu.
    - D. ((Hamzatul-ƙaɗ'i da hamzatul-wasli)), da ((at-taa'ul-marbuɗa)), da kuma ((Allamul-ƙamariyyah da allamush-shamsiyyah)); saboda a samu tantancewa tsakanin masu kama da juna a rubutu amma kuma sunada banbanci da juna wurin karantawa.
    - E. ((Al-madduɗ-ɗabi'ee)); saboda yawanta a cikin yaren Larabci da kuma buƙatuwar ɗalibi ga saninta.
    - F. ((Harafin alif wanda yake zuwa bayan wawul-jama'a)); domin nuni zuwa ga cewa wannan harafin wawun ɗin na jam'i ne; don kada a karantashi a matsayin alif.
    - G. ((yarukan da ake amfani dasu wurin rubutun Alƙur'ani)): Kuma na rubuta misalansu da irin rubutun Alƙur'ani; domin ɗalibi ya karanta Alƙur'ani batareda ya cakuɗa shi da abinda ya koya na ƙa'idojin karatu ba.
    - H. Lambobi: daga lamba ta ((0-20)); saboda ɗalibi ya iya karatun ɗai-ɗaikun lambobi da kuma masu goyo.
11. Na rarraba babin ((Karatun kalmomi)) zuwa darrussa biyar: Tun daga kalmomi biyu zuwa kalmomi huɗu, sa'annan sai karatun jumla, sai kuma karatun magana wacce aka ginata daga jumloli da yawa..

12. Na fara darrussan daga wasali sama sa'annan wasali ƙasa sai kuma rufu'a -saboda wasalin sama shine mafi sauƙin wasulla a furtawa sai wasali ƙasa yana binsa baya a sauƙi- daga nan sai na biyo baya da darasin ɗauri.

13. A babin ((Haruffa masu wasulla da ɗauri)) na taƙaita misalai ne akan haruffa guda uku kaɗai.

14. A farkon babi na biyu zuwa babi na biyar, na sanya dukkan baƙaƙen haruffan larabci tareda darussansu da ake buƙatan yi tareda misalai.

15. Na yi wasullan dukkan kalmomi, kuma na ɗora wasulla biyu akan harafin Alif.

16. Na taƙaitu da buga misalai daga kalmomin Al-ƙur'ani mai girma da kuma Sunnar Annabi; don sune ginshiƙin yaren Larabcin

17. Wurin zaɓar misalai, na kula da kasancewarsu misalai ne masu sauƙin karantawa da fahimta kuma masu ma'ana a fili.

18. Wurin zaɓar misallai a babin ((Karantun Kalmomi)): nayi amfani da kalmomi dasuke ƙunshe da ma'anoni na aƙida da ladubba da halaye na ƙwarai; don ɗalibi ya haɗa tsakanin ilimi da tarbiya.

19. Tun daga babin farko har zuwa babi na biyar, na jera haruffan da ake buƙatar koyonsu kamar yanda suke a jerin haruffan larabci, amma daga nan, jerin ya kasance ne ko dai kafin harafin da ake buƙatar koyonsa ko kuma a bayansa.

20. Ban mai-maita wata kalma ɗaya ba a cikin misalai; saboda ɗalibi ya samu damar karanta kalmomi mabanbanta.

21. Na rarraba haruffa da misalai ne a cikin gidaje, kuma nayi amfani da launin fari da kore wurin banbantawa tsakanin layukan su.

22. Nayi amfani da launi ja wurin rarrabewa tsakanin haruffa da wasullan da ake nufin koyarwa.

23. Nayima littafin Manhaja ta zamani tareda sautin haruffansa da kalmominsa; don ɗalibi ya samu ƙwarewa ta hanyar saurare kuma ya iya karatu mai kyau.

24. Bayan wannan littafin, na rubuta wani littafi na musamman akan koyon rubutu wanda na sanyama suna da: (Al-ƙa'idatul-madaniyyah - don karantar da rubutun Larabci ga ƴan koyo-); saboda ɗalibi ya haɗa ƙwarewar karatu da rubutu.

***

## Ababen da Al-ƙa'idatul-madaniyyah tayi fice da su

1. An ginata ne gini na ilimi daga littaffan yaren Larabci.
2. Ta ƙunshi dukkan ƙa'idojin karatu.
3. Sauƙi wurin koyarda karatu.
4. Bin matakai ahankali wurin koyarda karatu.
5. Koyon karatu da ƙwarewa a cikin gajeren lokaci.
6. Misalanta daga Alƙur'ani da Sunnar Annabi aka ɗauko su.
7. Misalai masu sauƙi da bayyananiyar ma'ana.
8. Rashin mai-maita misalai.
9. Misalan dake cikin babin ((Karatun kalmomi)): suna ƙunshe da Aƙida da halaye na ƙwarai.
10. Tanada manhaja ta zamani wanda yake taimakawa wurin saurare da kuma karatu ingantacce.
11. A bayanta akwai littafin dake koyarda rubutu da irin misalan da suke cikin na karatu.

***


# MANUFOFIN AL-ƘA'IDATUL MADANIYA

**Bayan sauke wannan littafin, ɗalibi zai wayi gari -da izinin Allah- yana iya:**

- Gane baƙaƙen haruffan larabci da yanda suke zuwa daban-daban.
- Iya karanta baƙaƙen haruffan larabci karatu lafiyayye da kuma duk yanda suke kasancewa.
- Zai san wasulla da ɗauri.
- Zai iya karanta haruffa da wasulla da ɗauri.
- zai san wasulla biyu.
- Zai samu iya karanta haruffa masu wasulla biyu.
- Zai san haruffa masu shadda da wasulla.
- Zai iya karanta haruffa masu shadda tareda wasulla da kyau.
- Zai san haruffa masu shadda da wasulla biyu.
- Zai iya karanta haruffa masu shadda tareda wasulla biyu da kyau.
- Zai iya rarrabewa tsakanin Alhamzatul- ƙaɗ'i da ta Alhamzatul-wasl a cikin karatu da rubutu.
- Zai san haruffan Almadduɗ-ɗabi'ee.
- Zai gane alif wanda yake zuwa bayan wawul al-jama'a
- Zai gane takuri yayin wucewa da yayin yin waƙafi.
- Zai iya karanta allamul-ƙamariyyah da kuma allamush-shamsiyyah da kyau.
- Zai ƙware a karatun kalmomi da jumloli da maganganu da kyau.
- Zai iya karanta Alƙur'ani ta hanyar rubutun Rasmul-uthmaniy.
- Zai ƙware wurin karatun lambobi da kyau.

***

## TASWIRAR BAYANIN TSARIN KARATU




**BABI NA ƊAYA**
Baƙaƙen Haruffan Larabci

**BABI NA BIYU**
Haruffa da wasulla da ɗauri

**BABI NA UKU**
Haruffa masu wasulla biyu

**BABI NA HUƊU**
Haruffa masu shaddah da wasulla

**BABI NA BIYAR**
Haruffa masu shaddah tareda wasulla biyu

**BABI NA SHIDA**
Hamzatul-ƙadʾi da Hamzatul-wasl

**BABI NA BAKWAI**
Madduɗ-ɗabi’ee

**BABI NA TAKWAS**
Alif dake zuwa bayan wawul-jama’a

**BABI NA TARA**
TAKURI

**BABI NA GOMA**
Allamul-ƙamariyyah da Allamush-shamsiyyah.

**BABI NA GOMA SHA ƊAYA**
Karatun Kalmomi

**BABI NA GOMA SHA BIYU**
Alamomi da yaren da ake amfani dashi wurin rubutun Alƙur’ani.

**BABI NA GOMA SHA UKU**
Lambobi

# SHIMFIƊA

## ZUWA GA MALAMI

Adadin haruffan (28) ne, kuma kowane harafi akwai yanda ake rubuta shi da suna da sauti; ga bayani akan haka:

| Yanda ake rubuta harafi | Sunansa [1] | Sautinsa |
|---|---|---|
| أ [2] | Alif | A |
| ب [3] | Ba | Ba |
| ت | Ta | Ta |
| ث | Tha | Tha |
| ج | Jim | Ja |
| ح | Ha | Ha |
| خ | Kha | Kha |
| د | Dal | Da |
| ذ | Zhal | Zha |
| ر | Ra | Ra |
| ز | Za | Zaa |
| س | Siin | Siin |
| ش | Shin | Shiin |
| ص | Swad | Swad |

| Yanda ake rubuta harafi | Sunansa | Sautinsa |
|---|---|---|
| ض | Dhad | Dha |
| ط | Ɗwa'un | Ɗwa |
| ظ | Zwa | Zwa |
| ع | A'een | A'een |
| غ | Gha | Ga |
| ف | Faa | Faa |
| ق | Qwaf | Qwa |
| ك | Kaf | Ka |
| ل | Lam | La |
| م | Mim | Ma |
| ن | Nun | Na |
| هـ | Ha | Ha |
| و | Waw | Wa |
| ي | Ya | Ya |

1-Sunayen haruffa ana karantasu ne da ɗaurin harafin ƙarshe, haka ma lokacin wucewa da karatu, da kuma tanwinin ruf`ah.

2-Alif harafi ne mai sauƙin faɗi kuma mai ɗauri, harafin dake kafinsa ya kasance mai fat`ha ne (wasali sama), shi yasa sautinsa baya bayyana sai dai idan an karanta shi da wani harafi kafinsa, misali (تَا – بَا) kuma tsawon sautinsa gwargwadon Harka biyu ne.

3-Sautinsa gwargwadon tsawon wasali ɗaya ne, haka ma sauran haruffan da ke biye masa.

***

BABI NA FARKO

# BAƘAƘEN LARABCI

## MANUFOFI

**Bayan kammala wannan babin, da izinin Allah ɗalibi zai wayi gari yana iya:**

- Gane baƙaƙen Larabci.
- karanta baƙaƙen Larabci da kyau.
- Gane yanda baƙaƙen larabcin suke zuwa wurare daban-daban.
- Karanta baƙaƙen Larabci duk yanda suka zo a wurare daban-daban da kyau.
- Gane harafin Alhamzah da yanda take zuwa daban-daban.
- San mece ce alhamzatul-mamduda kuma ya iya karanta ta.
- Ya san aliful-maƙsura kuma ya iya karanta ta.

***

TAMBIHI GA MALAMI

***Yanda ake karantawa**

**BAYANIN DARASI NA FARKO (Shafi na 15).**

Ɗalibi zai karanta sunan harafi kamar yanda aka bayyana a shinfiɗar da ta gabata (shafi na 11).

Misali: Harafin (ا) zai karanta shi ((Alif)), kuma Harafin (ب) zai karanta shi ((Baa)), Harafin (ج) zai karanta shi ((Jim)), kuma Harafin (ز) ya karanta shi ((Zaa)) haka nan sauran haruffa zai yi.

---

**BAYANIN DARASI NA BIYU (Shafi na 16).**

Ɗalibi zai karanta haruffan kamar yanda zuka kasance a wurare daban-daban, kamar dai yanda aka bayyana a shinfiɗar da ta gabata (shafi na 11).

Misalin wannan: Harafin Jimun dake iya zuwa a tsakiyar kalma da ƙarshenta wato (ـجـ – ج) duka za'a karanta sa ((Jim), haka nan a sauran baƙaƙen.

**TAMBIHI:** A wannan darasin ba'a faɗawa ɗalibi cewa: wannan harafin yana zuwa farkon kalma ko ƙarshenta; za'a taƙaita ne kawai ga sanar dashi yanda zai karanta harafin duk inda yazo kuma duk yanda aka rubuta sa.

---

**BAYANIN DARASI NA UKU (Shafi na 20).**

Duk inda harafin Alhamzah ta kasance -akan layi ko saman Alif ko ƙasansa, ko saman harafin wawun ko saman harafin ya'un (ء – أ – إ – ؤ – ـئـ – ئ)

A wannan darasin ɗalibi zai karanta ta ((hamzah)), Amma a sauran darussan zai karanta ta sautinta ne na « ءَ » “a”.

---

**BAYANIN DARASI NA HUƊU (Shafi na 20).**

**Al-Hamzatul-Mamduda** : ita ce wacce ake rubutawa a matsayin harafin Alif tareda alamar madda akanta (آ).

A wannan darasin ɗalibi zai faɗi sunanta ne yace ((Hamzatun-mamdudah)) amma a cikin sauran darussan zai karanta ta da sautinta ne na madda (( )).

**TAMBIHI:**

Idan harafin hamzah mai wasali sama ya kasance a farkon kalma kuma sai aliful maddi mai ɗauri ya biyo bayanta kamar misalin (أَاذَانٌ); a wannan yanayin ana rubuta ta (آذَانٌ) , ko kuma a tsakiyar kalma misali (رَأَاهُ) ana rubuta ta (رآهُ), da misalin kalmar (قُرْءَانٌ) ana rubuta ta ne (قُرْآنٌ).

---

**BAYANIN DARASI NA BIYAR (Shafi na 20).**

Al-aliful Maƙsura: Ana rubuta ta matsayin ya'un a ƙarshen kalma amma batare da ɗigo biyu ba (ruwa) guda biyu na ya'un ba.

A wannan darasin ɗalibi zai karanta sunanta ne yace ((alifun maƙsurah)) amma a sauran darussan zai karanta ta da sautinta ta ne (ا)

# DARASI NA FARKO
## Baƙaƙen Haruffan Larabci

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| ث | ت | ب | ا | |
| خ | ح | ج | | |
| ز | ر | ذ | د | |
| ض | ص | ش | س | |
| غ | ع | ظ | ط | |
| ل | ك | ق | ف | |
| ي | و | ه | ن | م |

## DARASI NA BIYU

**Yanda baƙaƙen haruffan larabci suke zuwa**

| | | | |
|---|---|---|---|
| ـا | ـا | ا | ا |
| ـب | ـبـ | بـ | ب |
| ة ـة ـت | ـتـ | تـ | ت |
| ـث | ـثـ | ثـ | ث |
| ـج | ـجـ | جـ | ج |
| ـح | ـحـ | حـ | ح |
| ـخ | ـخـ | خـ | خ |

| | | | |
|---|---|---|---|
| ـد | ـد | د | د |
| ـذ | ـذ | ذ | ذ |
| ـر | ـر | ر | ر |
| ـز | ـز | ز | ز |
| ـس | ـسـ | سـ | س |
| ـش | ـشـ | شـ | ش |
| ـص | ـصـ | صـ | ص |
| ـض | ـضـ | ضـ | ض |

| | | | |
|---|---|---|---|
| ـط | ـطـ | طـ | ط |
| ـظ | ـظـ | ظـ | ظ |
| ـع | ـعـ | عـ | ع |
| ـغ | ـغـ | غـ | غ |
| ـف | ـفـ | فـ | ف |
| ـق | ـقـ | قـ | ق |

| | | | |
|---|---|---|---|
| ـك | ـكـ | كـ | ك |
| ـل | ـلـ | لـ | ل |
| ـم | ـمـ | مـ | م |
| ـن | ـنـ | نـ | ن |
| ـه ه | ـهـ | هـ | ه |
| ـو | ـو | و | و |
| ـي | ـيـ | يـ | ي |

## DARASI NA UKU
## HAMZAH

ء | Yanda Hamzah take zuwa

| | | |
|---|---|---|
| ـإ إ | ـأ أ | ء |
| ـئ ئ | ـئـ ئـ | ـؤ ؤ |

## DARASI NA HUƊU
## Almazah Almamduda

آ | Yanda Almazah Almamduda take zuwa

| | |
|---|---|
| ـآ | آ |

## DARASI NA BIYAR
## Alif Almaƙsurah

ى | Yanda Alif Almaqsura yake zuwa

| | |
|---|---|
| ـى | ى |

BABI NA BIYU

# HARUFFA MASU WASULLA DA ƊAURI

## MANUFOFI

**Bayan kammala wannan babin, da izinin Allah ɗalibi zai wayi gari yana iya:**

- Gane wasulla da ɗauri
- Iya karanta haruffa tareda wasulla da ɗauri da kyau..

**Wasali:** wani ɗan zane ne ƙarami wanda ake ɗorawa saman harafi ko ƙasansa; domin a bayyana sautinsa.

**ALFAT`HA:** wani ɗan layi ne ƙarami a kan harafi (◌َ).

**AL-DWAMMA:** wata ƴar ƙaramar Wawun ce a saman harafi (◌ُ).

**AL-KASRA:** Wani ɗan layi ne ƙarami ƙasan harafi (◌ِ).

**AL-SUKUN:** Wani ɗan kewayayyen zane ne saman haraf (◌ْ).

---

*** YANDA AKE KARANTAWA:**

**Bayanin darussa na ɗaya, dana biyu dana uku (Shafi na 23, 26, 29)).**

Ɗalibi zai karanta sautin harafi ne tareda wasalinsa (أُ - إِ – أَ) kamar yanda aka bayyana sautinsa a shimfiɗar dake a shafi na ((11)).

---

**Bayanin misalan darussa na ɗaya, dana biyu dana uku (Shafi na 24, 27,30)).**

1. A ɗaki na farko: ɗalibi zai karanta sautin harafin tareda wasakinsa (أَ).
2. A ɗaki na biyu: ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasakinsa sannan ya karanta na biyu tareda wasalinsa (خَـ) sannan sai ya haɗesu yakaranta su tare yace (أَخَـ).
3. A ɗaki na uku: ɗalibi zai mai-maita abinda yayi a ɗaki na biyu sannan sai ya karanta harafi na uku tareda wasalinsa (ـذَ) sannan sai ya karanta kalmar baki ɗaya wato (أَخَذَ).
4. kamar haka ne dai ɗalibi zai ci gaba da karantawa a sauran misalan darasin wasalin ƙasa da Rufu'a.

---

**BAYANIN DARASI NA HUƊU (Shafi na: 32).**

Ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (أَ), sannan kuma sai ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai ɗauri, (أَبْ); saboda ba'a iya furta harafi mai ɗauri shi kaɗansa sai tareda haɗasa da wani.

---

**BAYANIN MISALAN DARASI NA HUƊU (Shafi na: 33).**

1. A ɗaki na farko: ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasakinsa (بَـ), sannan kuma sai ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai ɗauri (بَأْ).
2. A ɗaki na biyu: ɗalibi zai mai-maita abinda yayi a ɗaki na farko, sa'annan sai ya karanta harafi na uku tareda wasalinsa (سَ) , sai kuma ya sai furta kalmar baki ɗaya(بَأْسَ).

---

**TAMBIHI:**

Daga wannan babin har zuwa ƙarshen littafin, ɗalibi zai karanta sautin harafi ne tareda wasalinsa ko ɗauri, ba zai faɗi sunan harafin ne ba.

# DARASI NA FARKO
## WASALI SAMA (◌َ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثَ | تَ | بَ | أَ |
| دَ | خَ | حَ | جَ |
| سَ | زَ | رَ | ذَ |
| طَ | ضَ | صَ | شَ |
| فَ | غَ | عَ | ظَ |
| مَ | لَ | كَ | قَ |
| يَ | وَ | هَ | نَ |

**Misallan**
**wasali sama (َ)**

| | | |
|---|---|---|
| أَخَذَ | أَخَ | أَ |
| بَسَطَ | بَسَ | بَ |
| تَرَكَ | تَرَ | تَ |
| ثَبَتَ | ثَبَ | ثَ |
| جَمَعَ | جَمَ | جَ |
| حَمَلَ | حَمَ | حَ |
| خَتَمَ | خَتَ | خَ |
| دَخَلَ | دَخَ | دَ |

| | | |
|---|---|---|
| ذَهَبَ | ذَهَـ | ذَ |
| رَفَعَ | رَفَـ | رَ |
| زَعَمَ | زَعَـ | زَ |
| سَجَدَ | سَجَـ | سَـ |
| صَدَقَ | صَدَ | صَـ |
| عَبَسَ | عَبَـ | عَـ |
| غَفَرَ | غَفَـ | غَـ |
| نَزَلَ | نَزَ | نَـ |

# DARASI NA BIYU
## WASALI ƘASA (ِ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثِ | تِ | بِ | إِ |
| دِ | خِ | حِ | جِ |
| سِ | زِ | رِ | ذِ |
| طِ | ضِ | صِ | شِ |
| فِ | غِ | عِ | ظِ |
| مِ | لِ | كِ | قِ |
| يِ | وِ | هِ | نِ |

## Misalan wasali ƙasa (ِ)

| | | |
|---|---|---|
| يَئِسَ | يَئِـ | يَـ |
| أَجِدَ | أَجِـ | أَ |
| رَحِمَ | رَحِـ | رَ |
| بَخِلَ | بَخِـ | بَـ |
| رَدِفَ | رَدِ | رَ |
| شَرِبَ | شَرِ | شَـ |
| فَزِعَ | فَزِ | فَـ |
| نَسِيَ | نَسِـ | نَـ |

| | | |
|---|---|---|
| خَـ | خَشِـ | خَشِيَ |
| خَـ | خَطِـ | خَطِفَ |
| مَـ | مَعِـ | مَعِيَ |
| سَـ | سَفِـ | سَفِهَ |
| بَـ | بَقِـ | بَقِيَ |
| عَـ | عَلِـ | عَلِمَ |
| سَـ | سَمِـ | سَمِعَ |
| شَـ | شَهِـ | شَهِدَ |

# DARASI NA UKU
## RUFU'A (ُ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثُ | تُ | بُ | أُ |
| دُ | خُ | حُ | جُ |
| سُ | زُ | رُ | ذُ |
| طُ | ضُ | صُ | شُ |
| فُ | غُ | عُ | ظُ |
| مُ | لُ | كُ | قُ |
| يُ | وُ | هُ | نُ |

## Misallan

### Rufu'a (ُ)

| | | |
|---|---|---|
| كَبُرَ | كَبُـ | كَـ |
| كَثُرَ | كَثُـ | كَـ |
| ثَخُنَ | ثَخُـ | ثَـ |
| يَدُكَ | يَدُ | يَـ |
| قَرُبَ | قَرُ | قَـ |
| حَسُنَ | حَسُـ | حَـ |
| بَصُرَ | بَصُـ | بَـ |
| عَضُدَ | عَضُـ | عَـ |

| | | |
|---|---|---|
| طُبِعَ | طُبِـ | طُـ |
| ظُلِمَ | ظُلِـ | ظُـ |
| عُفِيَ | عُفِـ | عُـ |
| فُتِحَ | فُتِـ | فُـ |
| قُرِئَ | قُرِ | قُـ |
| كُبِتَ | كُبِـ | كُـ |
| هُدِيَ | هُدِ | هُـ |
| وُضِعَ | وُضِـ | وُ |

# DARASI NA HUƊU
## ƊAURI (◌ْ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| أَثْ | أَتْ | أَبْ | بَأْ |
| أَدْ | أَخْ | أَحْ | أَجْ |
| أَسْ | أَزْ | أَرْ | أَذْ |
| أَطْ | أَضْ | أَصْ | أَشْ |
| أَفْ | أَغْ | أَعْ | أَظْ |
| أَمْ | أَلْ | أَكْ | أَقْ |
| أَيْ | أَوْ | أَهْ | أَنْ |

## Misallan
## Ɗauri (◌ْ)

| | |
|---|---|
| بَأْسَ | بَأْ |
| سَبْعَ | سَبْ |
| أَجْرُ | أَجْ |
| يَدْعُ | يَدْ |
| عَرْشَ | عَرْ |
| نَصْرُ | نَصْ |
| فَضْلُ | فَضْ |
| بَطْشَ | بَطْ |

| | |
|---|---|
| بَعْـضُ | بَعْـ |
| مَكْـرُ | مَكْـ |
| قَلْـبِ | قَلْـ |
| أَمْـرُ | أَمْـ |
| كُنْـتَ | كُنْـ |
| أَهْـلُ | أَهْـ |
| يَوْمَ | يَوْ |
| غَيْـبُ | غَيْـ |

BABI NA UKU

# HARUFFA MASU WASULLA BIYU

## MANUFOFI

**Bayan kammala wannan babin, da izinin Allah ɗalibi zai wayi gari yana iya:**

- Gane Wasulla biyu.
- Karanta haruffa masu wasulla biyu da kyau.

## TAMBIHI GA MALAMI

AT-TANWIN: (Wata nunun ce mai ɗauri wacce ake ƙarawa, tana kasancewa ne a ƙarshen suna a lokacin furta sa, amma bata bayyana a lokacin rubutawa ko yayin tsayawa a karatu.

AL-FAT`HATAAN: Wasu ƴan layuka ne ƙanana dake zuwa saman harafin ƙarshe (ً) .

AL-KASRATAAN: Wasu ƴan layuka ne ƙanana a ƙasan harafin ƙarshe (ٍ) .

AL-ƊWAMMATAAN: Wasu haruffan Wawun ne ƴan ƙanana a saman harafin ƙarshe (ٌ) .

---

*** YANDA AKE KARANTAWA:**

**BAYANIN DARUSSA NA ƊAYA DANA BIYU DANA UKU (Shafi na 37, 39, 41).**

Ɗalibi zai karanta sautin harafin mai wasulla biyu (ءٌ - ءٍ – ءاً).

---

**BAYANIN MISALAN DARUSSA NA ƊAYA DANA BIYU DANA UKU (Shafi na: 38, 40, 42)**

1. Ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (عِـ), sa'annan kuma sai ya karanta harafin na biyu tareda wasalinsa, (نَـ), sa'annan sai ya haɗe su tare yace (عِنَـ) sa'annan kuma sai ya karanta harafi na uku wanda yakeda wasulla biyu (باً), sa'annan sai ya karanta kalmar baki (عِنَباً).
2. Idan kuma harafi na biyu a cikin kalma ya kasance mai ɗauri ne: ɗalibi zai karanta harafin farko tarda wasalinsa (فَـ) sa'annan sai karanta harafin farkon tareda harafi na biyu mai ɗauri (فَوْ) sa'annan sai ya karanta harfi na uku mai wasulla biyu (زاً), sa'annan sai ya karanta kalmar baki ɗayanta (فَوْزاً).
3. Haka dai zai ci gaba da tafiya akai a cikin sauran misalan darussan wasulla biyu ƙasa da rufu'o'i biyu.

***

# DARASI NA FARKO

## WASULLA BIYU SAMA (ًً)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثاً | تاً | باً | ءاً |
| داً | خاً | حاً | جاً |
| ساً | زاً | راً | ذاً |
| طاً | ضاً | صاً | شاً |
| فاً | غاً | عاً | ظاً |
| ماً | لاً | كاً | قاً |
| ياً | واً | هاً | ناً |

## Misallan

**Wasulla biyu sama (ً)**

| | |
|---|---|
| مَقْتاً | عِنَباً |
| أَحَداً | مَرَحاً |
| خَيْـراً | أَذىً |
| كَأْساً | فَوْزاً |
| وَسَطاً | قَرْضاً |
| نَفْعاً | حِفْظاً |
| مُلْكــاً | آنِفاً |
| ثَمَناً | حَرَماً |

# DARASI NA BIYU

## WASULLA BIYU ƘASA (ٍ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثٍ | تٍ | بٍ | ءٍ |
| دٍ | خٍ | حٍ | جٍ |
| سٍ | زٍ | رٍ | ذٍ |
| طٍ | ضٍ | صٍ | شٍ |
| فٍ | غٍ | عٍ | ظٍ |
| مٍ | لٍ | كٍ | قٍ |
| يٍ | وٍ | هٍ | نٍ |

## Misallan

**Wasulla biyu ƙasa (ٍ)**

| | |
|---|---|
| لَهَبٍ | شَيْءٍ |
| عَبْدٍ | آيَةٍ |
| نَفْسٍ | سَفَرٍ |
| أَرْضٍ | فُرُشٍ |
| زَرْعٍ | رَهْطٍ |
| طَبَقٍ | جُرُفٍ |
| رَجُلٍ | فَلَكٍ |
| قَرْنٍ | قَوْمٍ |

## DARASI NA UKU
## RUFU’O’I BIYU (◌ٌ)

| | | | |
|---|---|---|---|
| ثٌ | تٌ | بٌ | ءٌ |
| دٌ | خٌ | حٌ | جٌ |
| سٌ | زٌ | رٌ | ذٌ |
| طٌ | ضٌ | صٌ | شٌ |
| فٌ | غٌ | عٌ | ظٌ |
| مٌ | لٌ | كٌ | قٌ |
| يٌ | وٌ | هٌ | نٌ |

## Misallan
## Rufu’o’i biyu (◌ٌ)

| | |
|---|---|
| حَرَجٌ | كُتُبٌ |
| زَيْدٌ | رَوْحٌ |
| إِنْسٌ | شَهْرٌ |
| زَيْغٌ | مَرَضٌ |
| إِفْكٌ | رِزْقٌ |
| آثِمٌ | عَدْلٌ |
| كُرْهٌ | عَيْنٌ |
| وَحْيٌ | لَهْوٌ |

BABI NA HUƊU

# HARUFA MASU SHADDA DA WASULLA

## MANUFOFI

**Bayan kammala wannan babin, da izinin Allah ɗalibi zai wayi gari yana iya:**

- Gane haruffa masu shadda da wasulla.
- Karanta haruffa masu shadda da wasulla da kyau.

## TAMBIHI GA MALAMI

HARAFI MAI SHADDA: Shine harafi mai ɗauri wanda wani harafin irinsa mai wasali ya biyo bayansa, misali: (بّ = بَ + بْ).

SHADDA MAI WASALI SAMA: Ita ce wasu ɗan kawu nan harafin Sinun ƙanan ɗauke da wasali sama akai (ـَّ).

SHADDA MAI WASALI ƘASA: Ita ce wasu ɗan kawu nan harafin Sinun ƙanan ɗauke da wasali ƙasa ( ـِّ ).

SHADDA MAI RUFU'A: Ita ce wasu ɗan kawu nan harafin sinun ɗauke da rufu'a a sama. ( ـُّ ).

---

### YANDA AKE KARANTAWA:
### BAYANIN DARUSSA NA ƊAYA DA NA BIYU DA NA UKU

**((Shafi na 45, 47, 49).**

Ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (أَ) sa'annan sai ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai shadda (أَبَّ); domin ba'a iya furta harafi mai shadda shi kaɗai.

---

### Bayanin misalan darussa na ɗaya, dana biyu dana uku
### (Shafi na46, 48, 50)).

1. Ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (حَـ) sa'annan ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai shadda (حَبَّ) , sa'annan ya karanta harafi na uku da wasalinsa (ـةٍ) sa'annan sai ya karanta kalmar baki ɗaya (حَبَّةٍ).
2. Idan harafin dake bayan harafi na biyu mai shadda ya kasance harafi ne mai ɗauri: ɗalibi zai karanta harafin farkon tareda wasalinsa (يَـ) , sai ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai shadda da wasullansu (يَسَّـ) , sa'annan sai ya karanto harafin farko tareda na biyu mai shadda da wasullansu kuma ya haɗesu da harafi na ukku mai ɗauri (يَسَّرْ).
3. Haka dai zai ci gaba da yi idan harafin dake bayan harafi na biyu mai shadda ya kasance aliful-maƙsura ne, misali: (حَتَّى).
4. Idan harafi mai shadda ya kasance a ƙarshen kalma ne: ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (أَ), sa'annan ya karanta harafi na biyu da wasalinsa (عَـ), sai ya game su tare (أَعَـ) , sa'annan sai ya karanta harafi na biyu tareda harafi na ukku mai shadda da wasullansu (عَدَّ), sa'annan sai ya karanta kalmar baki ɗaya (أَعَدَّ).

***

## DARASI NA FARKO

**SHADDAH TAREDA WASALI SAMA ( ّ )**

| | | | |
|---|---|---|---|
| أَجَّ | أَثَّ | أَتَّ | أَبَّ |
| أَذَّ | أَدَّ | أَخَّ | أَحَّ |
| أَشَّ | أَسَّ | أَزَّ | أَرَّ |
| أَظَّ | أَطَّ | أَضَّ | أَصَّ |
| أَقَّ | أَفَّ | أَغَّ | أَعَّ |
| أَنَّ | أَمَّ | أَلَّ | أَكَّ |
| أَيَّ | أَوَّ | أَهَّ | |

**Misallan**

**shaddah tareda wasali sama ( ّ )**

| | |
|---|---|
| حَتَّى | حَبَّةٍ |
| سَخَّرَ | كَثَّرَ |
| كَذَّبَ | أَعَدَّ |
| عِزَّةٍ | حَرَّمَ |
| حِطَّةٌ | أَحَسَّ |
| أَحَقَّ | خَفَّفَ |
| سَلَّمَ | فَكَّرَ |
| بَوَّأَ | جَنَّةٌ |

# DARASI NA BIYU

## SHADDAH TAREDA WASALI ƘASA( ِّ )

| | | | |
|---|---|---|---|
| أَجِّ | أَثِّ | أَتِّ | أَبِّ |
| أَذِّ | أَدِّ | أَخِّ | أَحِّ |
| أَشِّ | أَسِّ | أَزِّ | أَرِّ |
| أَظِّ | أَطِّ | أَضِّ | أَصِّ |
| أَقِّ | أَفِّ | أَغِّ | أَعِّ |
| أَنِّ | أَمِّ | أَلِّ | أَكِّ |
| أَيِّ | أَوِّ | أَهِّ | |

## Misallan

**Shaddah tareda wasali ƙasa ( ِّ )**

| | |
|---|---|
| سَبِّحِ | عُجِّلَ |
| يُؤَدِّ | عُذِّبَ |
| بُرِّزَ | يَسِّرْ |
| بَشِّرِ | حُصِّلَ |
| عُطِّلَ | نُوَفِّ |
| ذُكِّرَ | كُلِّمَ |
| عَمِّكَ | مَهِّلِ |
| غُدُوِّ | زُيِّنَ |

# DARASI NA UKU

**Shaddah tareda Rufu'a ( ُّ )**

| | | | |
|---|---|---|---|
| أَجُّ | أَثُّ | أَتُّ | أَبُّ |
| أَذُّ | أَدُّ | أَخُّ | أَحُّ |
| أَشُّ | أَسُّ | أَزُّ | أَرُّ |
| أَظُّ | أَطُّ | أَضُّ | أَصُّ |
| أَقُّ | أَفُّ | أَغُّ | أَعُّ |
| أَنُّ | أَمُّ | أَلُّ | أَكُّ |
| أَيُّ | أَوُّ | أَهُّ | |

**Misallan**
**shaddah tareda rufu'a ( ُّ )**

| | |
|---|---|
| مِتُّ | يَبُثُّ |
| حِجُّ | يُرَدُّ |
| تَلَذُّ | تَمُرُّ |
| تُعِزُّ | يَمَسُّ |
| أَهُشُّ | نَقُصُّ |
| يَحُضُّ | يَدُعُّ |
| أَشَقُّ | يَحِلُّ |
| مُتِمُّ | يَظُنُّ |

BABI NA BIYAR

# HARUFFA TAREDA SHADDA DA WASULLA BIYU

## MANUFOFI

**Bayan kammala wannan babin, da izinin Allah ɗalibi zai wayi gari yana iya:**

- Gane haruffa masu shadda da wasulla biyu.
- Karanta haruffa masu shadda da wasulla biyu da kyau.

**TAMBIHI GA MALAMI**

SHADDA DA WASULLA BIYU SAMA: Wasu ƴan kawunan harafin sinun ne ƙanana ɗauke da wasulla biyu akai (ً).

SHADDA DA WASULLA BIYU ƘASA: Wasu ƴan kawunan harafin sinun ne ƙanana ɗauke da wasulla biyu a ƙasa ( ٍ ).

SHADDA TAREDA RUFU'O'I BIYU: Wasu ƴan kawu nan harafin sunun ne ɗauke da rufu'o'i biyu a sama ( ٌ ).

---

**YANDA AKE KARANTAWA:**
**BAYANIN DARUSSA NA ƊAYA DA NA BIYU DA NA UKU**
**((Shafi na 53, 55, 57).**

Ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (أَ) sa'annan kuma sai ya karanta harafin na farko tareda harafi na biyu mai shadda da wasulla biyu (أَبًّا).

---

**BAYANIN MISALAN DARUSSA NA ƊAYA DA NA BIYU DA NA UKU**
**(Shafi na 54, 46, 58))**

Idan kalma ta kasance mai haruffa uku ce: ɗalibi zai karanta harafin farko tareda wasalinsa (قَـ), kuma ya karanta na biyu da wasalinsa (ـوِ) , sa'annan sai ya haɗesu ya karanta su tare (قَوِ) , sa'annan sai ya karanta harafi na biyu tareda na uku wanda keda shadda da wasulla biyu (ـوِيًّا), sa'annan sai ya karanta kalmar baki ɗaya (قَوِيًّا).

---

**BAYANIN DARASI NA HUƊU (Shafi na: 59).**

Idan aka samu haruffa biyu masu shadda jere da juna a cikin kalma: ɗalibi zai karanto daga farkon kalmar zuwa kan harafi mai shadda na farko kamar yanda bayani ya gabata, sa'annan kuma sai ya karanta harafin na farko mai shadda tareda wanda yake gabaninsa, sa'annan sai ya ƙara karanto kalmar daga farkonta tareda harafin mai shadda na farko, sa'annan sai ya karanta haruffan biyu masu shadda tareda harafin dayake a gabaninsu, sa'annan kuma sai ya ƙara karanto kalmar tun daga farkonta tareda haruffan biyu masu shadda.

---

